UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

# YI BIDIYO MAI KYAU DA BABBAR WAYAR KA TA ZAMANI

KO ZA KA SO KA TATTAUNA DA WANI WANDA YAKE BIRGE KA A GARIN KU?

KO ZA KA SO ƊAUKAR BIDIYON WANI BIKI DON RABAWA SAURAN MUTANE? GA WASU SHAWARWARI DON TAIMAKA MAKA DA YIN BIDIYO DA WAYAR KA CIKIN SAUKI

## MATAKI NA 1: NEMI MAUDU'IN KA

- Bidiyo sako ne wanda muke so mu nuna ta hanyar hotuna. Kafin yin bidiyo, shirya tunanin ka kuma ka yi tunani akan sakon da kake so ka bayar.
- Wanene zai damu da batun? Wanene zai iya magana akai?

## MATAKI NA 2: SAITA ABINDA ZA'A DAUKA A TSAKIYAR MAHANGAR

- Zaɓi wurin da ya dace inda ba za'a dame ka ba ( wucewar motoci, horn na mota ...)
- Yi bidiyon tare da haske a bayan ka (rana, fitila...) saboda hasken ya nuna akan mutanen da kake bidiyon su.

## MATAKI NA 3: DUBA YAWAN MEMORI A WAYAR

- Kada ka manta cewa akwai isasshen memori akan wayar.
- Galibi, manhajoji, bidiyo da sauti suka fi cin yawan memorin waya.

## MATAKI NA 4: ƊAUKAR BIDIYO!

- Ɗauki bidiyon a kwance. Bidiyon ka zai zama a tsarin 16/9 kuma za'a a kalle shi a cikakken allo.
- Kula da motsi. Idan kayi motsi da yawa, hoton zai yi rawa kuma yayi wahalar kallo. Tuna da riƙe wayar ka da kyau, idan zai yiwu, da dukkan hannaye.



Plus d'outils
et de conseils
pour communiquer avec les communautés sur le site :
cwc.westafrica.exposed